Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Absolute Truth 2." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-1041-1-tabbat-haqiqan-2/.

# Tabbat Haqiqan 2

[Page 1]

Bismi l-Lāhi al-Raḥmāni al-Raḥīm, ṣalla l-Lāhu ʿalā man lā nabiyya baʿdahu

Gode Allahu Mai Sarauta ḥaqīqan Wanda ya yi ma kowa tabbat ḥaqīqan

Mu yi Ṣalāti da sallama bisa fiyayye Ahmadu ya fi kowa tabbat ḥaqīqan

Duk ku saurara za ni waƙa ku tuba Don ku samu ku tsira tabbat ḥaqīqan

Wanda bai girgiza ma Sarkin Musulmi Shi ka mutu da Jahlu tabbat ḥaqīqan

Wanda dai ya ƙi bin hukunci da ya yi Ba shi Hujja ga gobe tabbat ḥaqīqan

Wanda ya zam imamu ya yi ko adalci Shi adda yalwa ga gobe tabbat ḥaqīqan

Wanda ya zam imamu don cutar mutane Shi wuta kan ci gobe tabbat ḥaqīqan

Masu aza dukiya garin bin sarauta Babu shakka su ƙuna tabbat ḥaqīqan

Wanda ya zama hakimi ya yi raḥma Shi ka tsira ga gobe tabbat ḥaqīqan

[Page 2]

Ai fa in ya zamo da tsanani da wahala Shi ka wahala ga gobe tabbat ḥaqīqan

Masu matsawa talaka kuwa don sarauta Su kama tsuwa ga gobe tabbat ḥaqīqan

Masu ƙin hakiminsu dan ba shi ba su Suka ƙuna ga gobe tabbat ḥaqīqan

Masu kafa tattashi suna so gabana Kausara Allah ka ba su tabbat ḥaqīqan

Masu yawon gari suna yin fasadi Su ka yawon wuta fa tabbat ḥaqīqan

| | |
|---|---|
| Masu kangara kururuwa dudda sara | Suka kuka ga gobe tabbat ḥaqīqan |
| Wanda alƙali ya kirai ya ƙi karɓa | Shi wuta kan kirashi tabbat ḥaqīqan |
| Hakana wanda ya ƙi ko bin hukumci | Wanda alƙali ya yi tabbat ḥaqīqan |
| Ai fa alƙali in fa ya sake hukumci | Kāfiri na ga 'Amdu tabbat ḥaqīqan |
| Masu hana nasu zuwa inda ḥukmu | Gobe za su zo wuta fa tabbat ḥaqīqan |

[Page 3]

| | |
|---|---|
| Wanda ya walwale hukumcin sharī ʿa | Shi da kulki ga gobe tabbat ḥaqīqan |
| Mai abota da za shi shawo 'azaba | Can ga bautan wuta fa tabbat ḥaqīqan |
| Masu ƙwacen ƙasa suna nuna ƙarfi | Suka ɗaukatta gobe tabbat ḥaqīqan |
| Masu cin dukiya ta Baital wasunsu | Su wuta kan ci gobe tabbat ḥaqīqan |
| Haka na masu cin gululu su ɓoye | Gobe an bayyana su tabbat ḥaqīqan |
| Dud da ku masu yin bugu dut su kimtse | Gobe an bubbuge su tabbat ḥaqīqan |
| Masu kushen awon da ya fara kamuwa | Su wuta kanfa ƙone tabbat ḥaqīqan |
| Masu kira da a yi rabo da Khumusi ga yaƙi | Su wuta kan fa kwashe tabbat ḥaqīqan |
| Haka na masu yin fushi ko musulmi | Au amana su ƙuna tabbat ḥaqīqan |

[Page 4]

| | |
|---|---|
| Haka na masu cin amana ga gobe | Ba amana gare su tabbat ḥaqīqan |

| | |
|---|---|
| Masu kashe ciniki tsakanin musulmi | Gobe za su zo wuta fa tabbat ḥaqīqan |
| Masu ɓarna ga kasuwa dud da feƙi | Su wuta kan fa feƙe tabbat ḥaqīqan |
| Har miyagu da ke zina masu tarbe | Duw wuta za su gobe tabbat ḥaqīqan |
| Hakimai masu yin faɗa can ga zakah | Gobe ana zakkacesu tabbat ḥaqīqan |
| Masu rabawa sa ɗakunsu kwana | Duw wuta arrabonsu tabbat ḥaqīqan |
| Haka na wanda yaƙi daidaita kwana | Gobe ana karkatashi tabbat ḥaqīqan |
| Masu ɗaurin miji su ƙulla a kurce | Su a kan ɗaure gobe tabbat ḥaqīqan |
| Dud da matan ɗake fita ba lalura | Ba su tsere wuta fa tabbat ḥaqīqan |
| Haka na mace me akoncin kiwonshi | Gobe ana zallalla ta tabbat ḥaqīqan |

[Page 5]

| | |
|---|---|
| Aɗɗabibai (Hatsabibai) da masu kurce miyagu | Duw wuta za su gobe tabbat ḥaqīqan |
| Mai fa roƙo da ya fayye gobe fuska | Tai ana karkareta tabbat ḥaqīqan |
| Annamimi da ke rabawan Musulmi | Shi da al-Janna babu tabbat ḥaqīqan |
| Du da kai mai shiga tsakanin zumunta | Duw wuta za su ƙuna tabbat ḥaqīqan |
| Masu ƙarya da al-Walī shi a ba su | Dukiya duk su ƙuna tabbat ḥaqīqan |
| Du faɗata da anka ce gaskiya ta | Sai a raḥma da ceto tabbat ḥaqīqan |
| Nan fa waƙar ta cika aifa ramzi | Jumma Rushdin ka lura tabbat ḥaqīqan |

Ya jama'a mu tuba don wanda Ya yi tuba shi tsira tabbat ḥaqīqan

Duk mu gode Ubangiji mu yi salla Bisa Muhammada tabbat ḥaqīqan

Alḥamdu li l-Lāhi

Rabbi l- ʿālamīn

Āmīn!